# SUNAYEN LAQABI A AL'ADAR HAUSAWA

**Shamsuddeen Isma'ila da Muhammad Abubakar Zabi**
Sashen Hausa
Kwalejin Ilimi Ta Shehu Shagari, Sakkwato
Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya
Jami'ar Usmanu Danfodiyo Sakkwato
shamsuddeenismail83@gmail.com

***TSAKURE***
*Hausawa al'umma ce mai riqo da al'ada, wato Hausawa sun rayu a lokacin gargajiya bisa matakan rayuwa har guda uku. Ya fara tun daga haifuwa da aure da kuma mutuwa. A wannan mataki Hausawa sun yi amfani da sunaye iri-iri na gargajiya. Hatta bautarsu a gargajiya suka gudanar da ita a wancan lokaci. Haka kuma sun gudanar da rayuwa bayan karbar addinin Musulunci duk da haka ba su watsar da al'adunsu na gargajiya ba, wajen sanya wa ƴaƴansu laqabi irin nasu na gargajiya. Kuma sakamakon haduwarsu da Larabawa sun samu tasirin haduwa da su tafuskar Sunaye wanda ya qara samarwa Hausawa sunayen laqabi. A cikin wannan takarda za a dubi sunayen Hausawa lokacin gargajiya tare da sunayen lokaci da sanadi da yanayi da sunayen siffa. Sannan za a duba sunayen Hausawa bayan zuwan musulunci da sunayen asali da sunayen laqabi a al'dar Hausawa. A qarshe, kammalawa za ta biyo baya kafin manazartar takardar da za ta biyo baya.*

## 1. GABATARWA

Bincike ya nunu cewa al'ummar Hausawa al'umma ce mai riqo da al'ada, wato Hausawa sun rayu a lokacin gargajiya bisa matakan rayuwa har guda uku. Ya fara tun daga haifuwa da aure da kuma mutuwa. A wannan mataki Hausawa sun yi amfani da sunaye iri-iri na gargajiya. Har bautarsu a gargajiya da suke gudanar da ita a wancan lokaci. Haka kuma sun gudanar da rayuwa bayan karbar addinin Musulunci duk da haka ba su watsar da al'adunsu na gargajiya ba, wajen sanya wa ƴaƴansu laqabi irin nasu na gargajiya. Kuma sakamakon haduwarsu da Larabawa sun samu tasirin haduwa da su tafuskar Sunaye wanda ya qara samarwa Hausawa sunayen laqabi. Bayan zuwan turawan mulkin mallaka rayuwarsu ta gudana bisa sabon tsari. Duk da wadannan sauye-sauyen matakan rayuwa bai sa su Hausawa sun watsar da al'adunsu ba. Akwai hanyoyi da dama da za a iya duba ire-iren al'adun Hausawa, daya daga cikin hanyoyin ita ce hanyar nazarin sunayensu na gargajiya.
wanda suke amfani da shi tun matakin rayuwar farko har ya zuwa wannan zamani da kuma irin tasirin zamanin da aka samu a cikin harqar sunayen Hausawa a yau. Har ta kai masana da manazarta sun yi rubutu da dama a kan abin da ya shafi sunayen Hausawa jiya da yau. Abin da wannan bincike ke son zaqulowa shi ne sunayen laqabi a al'adar Hausawa.

## 2. WAIWAYE

Adamu, (2013) ya gabatar da takardarsa mai taken tasirin Musulunci a kan sunayen Hausawa. Sannan sai ya duba haifuwa a wajen Bahaushe da ranar zanen suna da sunayen Hausawa na gargajiya da kuma sunayen Hausawa bayan zuwan Musulunci daga qarshe kuma ya kawo sunayen sha'awa.

Shi kuma Ibrahim (1982) ya gabatar da kundin digirinsa na biyu mai taken dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci kan rayuwar Hausawa ta gargajiya. Bayan ya kawo gabatarwa sai ya kawo rayuwar Hausawa daga farko har zuwa yanzu. Yanda ya yi bayanin addinin gargajiya da kuma addinin musulunci, sai ya kawo sunayen Hausawa na gargajiya da kuma bayan zuwan musulunci. Daga qarshe ya rufe da bayanin matakan rayuwa Dan Adam.

Abbas, N. I. (2013) ya gabatar ta takardar sa mai taken Tasarifin Sunayen Hausawa na Gargajiya. Bayan ya kawo gabatarwa sai ya duba ma'anar suna da sunayen Hausawa da ma'anar tasarifi da kuma tasarifin sunayen Hausawa na Gargajiya. Sannan ya duba tsira a sunayen Hausawa, sai ya yi kammalawa.

### 2.1. Ma'anar Suna

Suna a ma'anar fannu yana nufin wata kebabbiyar kalma da wata al'umma ta yarda da ita domin kira ko ambaton wani mutum ko wata dabba ko tsirai ko wani abu mai rai ko maras rai (mace ko namiji) ta yadda za su bambanta da junansu ko makamantansu. Masana da manazarta sun tofa albarkacin bakin su game da ma'anar suna kamar haka: Garba (1990) cewa ya yi suna na nufi kalma da ake sa wa mutum ko wani abu don kiransa da shi. CNHN (2006) sun bayyana suna da cewa kalma ce da ake amfani da ita wajen kira ko ambaton wani abu. Bargery (1963) yace suna kalma ce da ake kiran mutum ko bukin da ake yi a rana ta bakwai ta haifuwar yaro ko yarinya a cikin al'ummar Hausawa. Abbas, (2013) suna kalma ce da ake amfani da ita wajen ambaton wani

abu, musamman don bambancewa da kuma rarrabawa. Daga wadannan bayanai, muna iya cewa suna wani abu ne da mutune suke saka wa wani abu mai rai ko maras rai domin kiransa da shi da tantancewa da bambantawa.

## 2.1 Sunayen Hausawa Lokacin Gargajiya

Hausawa mutane ne masu riqo da al'ada ainun. Wanda sun yi wata rayuwa kafin haduwarsu da baqi, suna amfani da wasu sunaye ne ta la'akari da abubuwa iriiri, wato suna la'akari ne da halin da haihuwa ta zo ko ta samu. Don haka za mu ga yadda kashe-kashen yake:

i- Sunayen Lokaci
ii- Sunayen Sanadi
iii- Sunayen Yanayi
iv- Sunayen Siffa

### *2.1.1 Sunayen Lokaci*

Irin wadannan sunaye sun shafi lokacin da aka haifi yaro ko yarinyar yana iya kasancewa kamar haka:

i- Dare
ii- Rana
iii- Hantsi
iv- Hazo
v- Damina

Duk irin wadannan sunaye a kan yi la'akari da wadannan lokuta domin saka wa abin da aka samu suna.

### 2.1.2 Sunayen Sanadi

Su kuma irin wadannan sunaye ana saka su ne sakamakon aukuwar wani abu, sai a yi la'akari da wannan abin a yi wa yaro suna. Misali

i- Mutuwa
ii- Gobara
iii- Fari
iv- Wani taro
v- Wadata

Wadannan sanadai duk ana amfani da su wajen samar wa yaran da aka Haifa suna a wani sanadi da ya faru daga cikin wadannan da aka lissafa a lokacin gargajiya.

### *2.1.3 Sunayen Yanayi*

Irin wadannan sunaye sun danganci lokacin da aka haifi yaron da kuma wane irin yanayi ya zo duniya. A kan yi amfani da irin wadannan yanayi ne domin rada wa yaro suna. Ga siffofin kamar haka:

i- Tagwaye
ii- Yaron da an fidda rai daga baya aka same shi
iii- Yaron da aka haifa da rigar haifuwa
iv- Yaron da aka haifa bayan tagwaye
v- Mace da namiji Tagwaye

### *2.1.4 Sunayen Siffa*

Irin wadannan sunaye Hausawa na rada wa yaransu ne ta la'akari da irin siffar da aka haifi jaririn da ita. Ga kadan daga cikin siffofin:

i- Yaron da aka haifa da qarin yatsa - Cindo
ii- Yaron da aka haifa ba gashi
iii- Yaron da aka haifa da farar fata
iv- Baqin yaro
v Yaron da aka haifa da qaramin jiki

## 3. Sunayen Hausawa Bayan Zuwan Musulunci

Samuwar addinin musulunci ga al'ummar Hausawa ya sanya sun sami sabuwar hanyar rayuwa wace ta qunshi Imani da Allah da ManzaninSa da kuma biyayya gare su bisa duk abin da suka bayyana. Wannan ta sanya rayuwar Hausawa ta canja kacokam suka karbi sabuwar rayuwa da ta canja yanayin zamantakewarsu da auratayya da bauta da ciniki da sauran mu'amala gaba daya ciki har da sunaye.

Samun sunaye bisa tsarin musulunci ya sanya Hausawa canza sunayensu zuwa na musulunci, don a ganinsu haka ya fi dacewa bisa sabuwar hanyar da ta zo musu. Saboda haka maimakon sunaye na gargajaya sai suka canja zuwa sunayen da addinin Musulunci ya zo da su. Amma duk da haka, ko da

suka sami sababbin sunayen, ba su dinga amfani da su yadda suka same su ba, sai da suka qirqiri nasu daga ciki ko kuma suka yi musu kwaskwarima ta yadda zai dace da harshensu.

**3.1 Sunayen Asali**

Rukunin wadannan sunaye ana kiransu na asali ne, domin sunaye ne da da ma akwai su a rayuwar Hausawa. Hausawa sun saba amfani da su a rayuwarsu ta yau da kullum (Abdullahi 2013). Wadannan sunaye sun wanzu tun lokacin da Hausawa suka karbi musulunci. Haka kuma wadannan sunaye sun yi tasiri ainu ga rayuwar Hausawa. Daga cikin wadannan sunaye akwai na yanka da kuma laqabi.

**3.2 Sunan Yanka**

Sunayen yanka, Sunaye ne da Hausawa suka samu daga addinin Musulnci. Sunaye ne da Hausawa Musulmi suke rada wa ýaýansu a ranar da ake yanka ragon suna (Abdullahi1997). A ranar wannan bikin na haifuwa ake rada irin wannan suna. Sunaye ne da Hausawa suka samu ko dai daga Alqur'ani ko Hadisi ko cikin tarihin Musulunci ko kuma ma'anar ta kasance abu mai kyau a harshen da aka saukar da addinin Musulunci (Abdullahi 2013). Ga sunaye da aka samu daga Sahabban Ma'aikin (S.A.W).

1- Abubakar
2- Umar
3- Usman
4- Aliyu

Babu shakka a qarqashin wadannan sunaye ana samu wasu sunayen yanka da na laqabi sakamakon cudanyar Hausawa da Larabawa ko kuma sakamakon karbar addinin Musulunci.

| Abubakar | Umar | Usman | Aliyu |
|---|---|---|---|
| 1- Garba | Sanda | Shehu | Ali |
| 2- Abu | Faruk | Usmanu | Alu |
| 3- Habu | Babuga | Modibbo | Gadanga |
| 4- Sadiq | Mani | Haidar | |
| 5- Garbati | Manu | Zaki | |
| 6- Garbu | Haido | Maisango | |
| 7- Garbai | Sarkin Yaqi | | |
| 8- Sahabi | | | |
| 9- Cika | | | |
| 10- Bukkar | | | |
| 11- Gagare | | | |
| 12- Sadauki | | | |
| 13- Buba | | | |
| 14- Bakari | | | |

**4. Dalilin Da Ke Haddasa Yi Wa Sunayen Musulunci Kwaskwarima Kafin A Mayar Da Su Laqabi A Al'adar Bahaushe**

Komai na rayuwar yana dalilin faruwa, ba haka kawai yake ba kasancewa ba. Haka yake a sunayen da Hausawa da suke mayar da sun alaqabi. Akwai dalilai kamar haka da suke haddasa kwaskwarima a sunayen yanka har su zama laqabi:

1- Sauqin fadi
2- Girmamawa
3- Zamananci

**5. SAUQIN FADI**

Wannan na nufin Bahaushe yana da dabi'ar duk abin da zai ba shi wahala wajen fadi to zai yi masa kwaskwarima domin ya dace da bakinsa ko furucinsa. To a sunayensa ma akwai irin wadannan ga misali:

***Abubakar*–** Abubakar suna ne da Musulunci ya zo da shi, amma da Bahaushe ya ga zai masa wahala ko wuyar fadi sai ya yi masa kwaskwarima ya mayar da shi Habu ko Abu.

***Adam***- Wannan suna ne da addinin Musulunci ya zo da shi kuma sunan Annabin Allah ne, Hausawa suka ga zai zamu musu mai wahalar fadi sai suka maya da shi Ado ko Ada koAdamu.

***Idrisu-*** Wannan ma suna ne da Hausawa suka samu daga addinin Musulunci kuma suna Annabi ne, wanda Hausawa suka ga zai yi musu wahalar fadi sai suka yake wasu harufa suka maida shi Idi.

***Salihu-*** haka yake wajen suna salihu Hausawa sun samo shi ne sakamakon zuwa Addinin Musulunci qasar Hausa, Hausawa sai suka yi wa suna kwaskwarima domin ya dace da furucinsu. Maimakon Salihu sai ya koma =Sale ko Salele.

***Ibrahim-*** Ibrahim suna ne da Hausawa suka sami shi sakamakon cu]anya da baqin larabawa wadanda suka zo da addinin Musulunci Hausawa suka ari sunan, amma da yake Bahaushe yana samarwa suna yanka laqabi ko kuma dan sauqin fadi sai ya mayar da Ibrahim Iro/Buraima/Ibro.

### 5.1 Girmamawa

Wannan na nufin ganin girma ko kimar wani abu, wanda daman Bahaushe yana da al'adar girmama na gaba da shi, don haka sau da yawa yakan sakaya sunan yanka ya yi masa wani laqabi da zai dinga kiran wannan sunan da shi. Misali ko sunan Manzanin Allah (S.W.A.) ko sunayen shugabanin addini ko kuma sunayen Iyayen mutum ko sunan sarke. Misalin sunan manzani Annabi Muhammadu Sallahu Laihi wassalam, wasu idan suka saka wa yaronsu suna sukan yi masa laqabi da Narasulu ko Tamadina ko Namariya da dai sauransu. Ta bangaren sunayen shugabanin addini kuma za ka ji ana cewa Amadu su kan yi masa laqabi da Tijjani saboda shehu Amadu Tijjani, kiran

suna Amadu sai ya zama kamar babu girmamawa a ciki. Haka kuma Bahaushe yana da al'ada sakaye sunan mahaifi ko shirki idan an saka wa yaro a gida za adinga fadin Babangida maimakon suna na ainihi, misali idan Muhammadu ko Umar sai a yi masa laqabi da Baba ko Babangida da sauran irin wa]annan don girmamawa.

### 5.2 Zamananci

Wannan kuma zamani ne kan zo da wannan yanayi wanda mafi yawancin rukunin samari ne da 'yan mata suka fi yin amfani da shi za a tara da suna ne maia kyau amma sai su mayar da shin a zamani misali kamar Garba – Garus ko Balkisu sai ya koma Billy Ko Tijjani sai ya koma Teejy ko Zainab Ya koma Zee ko Tukur ya koma TK da dai sauran makamatan haka.

## 6. KAMMALAWA

Jawaban da suka gabata hujja ce da za a qara amincewa da cewa Hausawa sun samu tasiri ainun haduwar su da Larabawa. Yadda gaba daya suka koma sunayen Musulunci, sakamakon Hausawa al'umma ce mai riqo da abin da suka yi imani da shi. Haka kuma binciken ya dan waiwayo sunayen Hausawa na gargajiya, sannan ya kawo sunan yanka a wajen Bahaushen zamani, sannan aka kawo sunaye da kuma dalilin da ke haddasa kwaskwarima a sunayen yanka na Bahaushe ya mayar da sun a laqabi, da suka samu daga sunayen da addinin Musulunci ya zo da shi.

## 7. MANAZARTA


Abbas, N. (2012). Nahawun Sunayen Hausawa. Kundin Digiri na biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usumanu Danfodiyo, Sakkwato.

Abdullahi, I.S.S. (2013). Li'irabin Sunayen Taurarin Littafin Ruwan Bagaja. Humanities In The Sub - Saharan: World UNICAIRO/ UMYUK Special Research in Humanities. Zaria, Nigeria: Ahmadu Bello University Press ltd, Zaria.

Abdullahi, I.S.S. (1997). Tasirin Zamani da Ilolinsa A Kan Sunayen Hausawa. Muqalar da aka gabatar a taron qarawa juna sani a tsangayar fasaha da addinin Musulunci. Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sakkwato.

Adamu, M. T. (2013). Tasirin Musulunci a kan Sunayen Hausawa. Takarda da aka gabatar A bikin Makon Hausa Na Dalibai Kwalejin Ilimi Ta Tarayya (F.C.E), Zariya.

Bargery, G. P. (1933). Hausa - English Dictionary and English - Hausa Vocabulary. London: Oxford University Press.

Bichi, A. Y. (2004). Sunayen Hausawa na gargajiya da ire-iren abincin Hausawa: Cibiyar nazarin harsunanan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Shuni, M. A. (2007). Bukin Suna A Garin Shuni. Kundin Digirin farko, Sashen Nazarin harsunan Nijeriya: jami'ar Usumanu Xanfodiyo, Sakkwato

Kano, B. U. (2006). Qamusun Hausa, Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.